
كتاب
الفقه الميسر
في ضوء الكتاب والسنة
إعداد
نخبة من العلماء

**FASSARAR**

# LITTAFIN FIKHUL MUYASSAR

NA BIYU

---

**Mai Fassara:**

Rufiayya Ɗalha

1442H=2020M

GABATARWA

Godiya ta tabbata ga Allah wanda ya bambanta maza da mata da yin haila da ɗaukar ciki.

Tsira da aminci su tabbata ga Annabi Muhammad da iyalansa da sahabbansa da wanda ya bi turbarsa har zuwa ranar sakamako.

Bayan haka; wannan shi ne fassarar littafin Fiﬁhul Muyassar na biyu da na fassara shi zuwa Hausa don kusantowa da ‘yan uwana mata muhimman hukunce-hukuncen da ya ﬁunsa, da suka shafe mu.

A ﬁarshe, ina roﬁon Allah ya karɓa min. Amin

‘yar uwarku a Musulunci.

Ruﬁayya Ɗalha

Rabi’ul Awwal, 1442H

Dai da

Oktoba, 2020M

Bismillahir Rahmanur Rahim

# DARASI NA FARKO

## Game Da Jinin Da Yake Fita Daga Mace

- Jini nawa ne yake fita daga mace?
- Jini uku ne yake fita daga mace, su ne: Jinin haila, jinin biki da jinin cuta.
- Mece ce Haila?
- Haila ita ce jinin da yake fita daga mahaifar mace idan ta balaga, a wasu kwanaki sanannu.
- Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata agare shi, da iyalansa ya ce da Hannatu 'yar Jahshi, ki yi hailarki kwana shida, ko kwana bakwai. Hakan sai ya zama shi ne galibin kwanakin jinin haila, kuma yana iya fiasa da haka ko ya fiaru.
- Mene ne Jinin Bifii?
- Jinin bifii shi ne jinin da yake fita daga gaban mace saboda haihuwa ko da abin da aka Haifa ɓari ne.
- Mene ne Jinin cuta?
- Jinin cuta shi ne ci gaban fitar jini daga gaban mace saboda rashin lafiya, ba a lokacin jinin haila, kuma ba a lokacin jinin bifii ba.

# DARASI NA BIYU

## Game Da Fara Jinin Haila Da Bayanin Siffofinsa

- Yaushe mata suka fara jinin haila?
- Farkon fara jinin haila ya kasance ne akan Hauwa'u matar Annabi Adamu, amincin Allah ya tabbata agare shi, bayan an sauko da su daga aljanna zuwa duniya. Sannan Allah ya hukunta shi akan 'ya'yan Annabi Adamu mata.

- Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata agare shi, da iyalansa ya ce, hafiifia, wannan wani al’amari ne da Allah ya hukunta shi akan ‘ya’yan Annabi Adamu mata.
- Mece ce sifar jinin Haila?
- Jinin haila bafii ne, mai wari, kuma fiazanta. Annabi tsira da amincin Allah su tabbata agare shi da iyalansa ya ce, hafiifia, jinin haila bafii ne yana fiarni, kuma Allah tsarkakakke maɗaukaki ya ce: “kuma suna tambayar ka game da jinin haila, ka ce da su fiazanta ne...”.
- Kuma jinin haila yakan zo ja ko fatsi-fatsi, mai bafii kuma a fiarshensa yakan canja ruwan fiasa.

DARASI NA UKU

Game Da Ambaton Abin Da Ake Sanin Zuwan Jinin Al’ada Da Shi Da Yankewarsa

- Da me ake sanin zuwan jinin haila?
- Ana sanin zuwan jinin haila ne da zubowarsa a lokacinsa, da kuma abin da yake riga shi wani lokaci na ciwon kai ko ciwon mara.
- Kuma da me ake sanin yankewarsa?
- Ana sanin yankewarsa da tsabtatar abin da aka toshe shi da shi,shi ne tsabtatar abin da mai haila take toshe gabanta da shi na auduga ko yanki don hana zubar jinin ko da zubar wani farin ruwa a fiarshen jinin a fiarshen haila shi ne ake kira da fiassa fara.

DARASI NA HUƊU

Game Da Maimaituwar Jinin Haila A Wata Ɗaya Da Abin Da Aka Faɗa Gameda Jinin Hailar Mai Ciki

- Shin jinin haila yana maimaituwa a wata ɗaya?
- Galibin mace tana jinin haila a kowane wata haila ɗaya, saura kwanakin watan kuma suna zama tsarki, sai dai ana samun wacce take jinin haila a wata sau biyu,

- Ko mai ciki tana jinin haila?
- Malamai sun yi saɓani game da jinin da wasu daga cikin mata suke gani a tsaka da lokacin ciki. Sai wasu daga cikinsu suka ce hafiifia shi jinin ne da hujjar afkuwarsa a sifar jinin haila ga wasudaga cikin mata kuma wasu daga cikinsu suka ce: Hafiifia shi ba jinin haila ba ne, a'a, shi jinin cuta ne domin shi jinin haila rushewar shirin mahaifa ne game da ɗaukar ciki, idan ciki ya samu sai a rasa jinin haila. Kuma saboda Hadisin da Imam Ahmad ya rawaito daga salim daga babansa cewa; Hafiifia ya saki matarsa alhali ta na jinin haila, sai Umar ya tambayi Annabi, tsira da amincin Allah su tabbata agare shi da iyalansa, game da haka. Sai Annabi, tsira da amincin Allah su tabbata agare shi da iyalansa, ya ce: "ka umarce shi da ya mayar da ita, sannan ya sake ta tana mai tsarki ko tana mai ciki".
- Sai ya sanya ciki ya zama alama, akan rashin jinin haila, kamar yadda ya sanya tsarki ya zama alama akan rashin sa.

DARASI NA BIYAR

Game Da Bayanin Mafi Yawancin Kwanakin Jinin Bifii

- Nawa ne mafi yawancin kwanakin jinin bifii?
- An karɓo daga Ummu-Salama, Allah ya yarda ita, ta ce: Mai jinin bifii ta kasance tana zama a lokacin Annabi, tsira da amincin Allah su tabbata agare shi da iyalansa, tsawon kwanaki arba'in".
- Kuma Imam Tirmizi, Allah ya ji fiansa, ya ce: Hafiifia Malamai da sahabbai da Tabi'ai da waɗanda suka biyo bayansu, sun haɗu akan cewa: Hafiifia mai jinin bifii tana barin salla tsawon kwana arba'in, sai dai idan mai jinin bifii ta ga tsarki kafin haka, to hafiifia za ta yi

wanka ta yi salla. Idan ta ga jinin bayan kwana arba’in, hafiifia mafi yawancin Malamai sun ce: ‘Ba za ta bar salla ba bayan kwana arba’in.’ Kuma shi ne maganar mafiya yawancin Malaman Fifiihu.

- Sai iyakacin kwana arba’in ya kasance shi ne galibin yawancin kwanakin jinin bifii.

DARASI NA SHIDA

Game da Hukunce-Hukuncen Jinin Haila da na Bifii

- Mene ne yake haramta saboda jinin haila da na bifii?
- Salla tana haramta saboda jinin haila da na bifii da Azumi da Ɗawafi da saduwa da saki a bisa haɗuwar Malamai.
- Kuma maganganun Malamai sun saɓa game da zama a Masallaci da taɓa Alfiur’ani da karanta shi, sai wasu daga cikinsu suka halatta haka, wasu kuma suka hana.
- Ko zaka ambata mana dalilan haramcin abubuwan da suka gabata?
- Amma haramcin salla, saboda jinin haila da na bifii. Saboda faɗar Annabi, tsira da amincin Allah su tabbata agare shi da iyalansa, ga Faɗima ‘yar Abi Hubaish. Idan haila ta zo, to kibar salla.
- Amma haramcin yin Azumi, saboda jinin haila da na bifii, saboda faɗar Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata agare shi da iyalansa, shi ashe ba idan ɗayarku tana jinin haila ba ta Azumi ba ta salla ba? Suka ce haka abin yake.
- Kuma dalilin haramcin yin Ɗawafi, saboda jinin haila da bifii faɗar Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata agare shi da iyalansa, ga Aisha lokacin da ta yi jinin haila tana mai harama da Aikin Hajji, ki aikata duk abin da mai Aikin Allah har sai kin samu tsarki.
- Kuma haramun ne saduwa da mai jinin haila da na bifii.

- Saboda faɗar Allah Maɗaukaki: “To ku fiauracewa mata a kwanakin jinin haila, kuma kada ku kusance su har sai sun samu tsarki”.
- Kuma saboda faɗar Annabi, tsira da amincin Allah su tabbata agare shi da iyalansa, lokacin da ayar ta sauka: “ku aikata komai da matanku, in ban da saduwar aure”.
- Abin da ake nufi da haka a sake su lokacin tsarkin da ba a sadu da su ba.
- Faɗakarwa:

Jinin bifii yana bambanta da na haila ne da kasancewar idda ba ta afkuwa da shi saboda iddar mai ciki tana fiarewa ne da haifar ciki.

- Allah Maɗaukaki ya ce: “mata masu ciki iddarsu shi ne su haife cikinsu”.

## DARASI NA BAKWAI

### Game da Bayanin Abin da Rama Shi Yake Wajaba da Abin da Rama shi ba ya Wajaba

- Mene ne rama shi yake wajaba akan mai jinin haila da na bifii?
- Rama Azumi ne yake wajaba akan mai jinin haila da na bifii.
- Rama salla ce ba ta wajaba akan mai jinin haila da na bifii.
- Kuma an karɓo daga Mu’azata, Allah ya yarda da ita, ta ce: Na tambayi Aisha sai na ce: Me ya sa mai jinin haila take rama Azumi kuma ba ta rama salla? Ta ce: Haka ya kasance yana faruwa da mu, muna tare da Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata agare shi da iyalansa, sai ya umarce mu da mu rama Azumi, kuma karmu rama sallah.

## DARASI NA TAKWAS

### Game da Abin da ya Halatta da Abin da Ake so Game da Mai Jinin Haila da na Bifii Tare da Mazajensu

- Ya halatta ga mai jinin haila da na bifii tare da mazajensu abinda zai zo:
- Ci da sha da bacci tare
- Wanke kan miji da taje shi.
- Mene ne ake so game da mai jinin haila da na bifii?
- Ana so ga mai jinin haila da na bifii fita don halartar idi tare dafiaurace wa salla.

DARASI NA TARA

Game da Hukunce-Huncen Jinin Cuta

- Mene ne hukuncin jinin cuta?
- Jinin cuta ba ya hana wani abu daga abubuwan da jinin haila da na bifii suke hanawa, kuma hafiifia mai jinin cuta hukuncintaɗaya da mace mai tsarki, tana salla, kuma tana Azumi, kuma tana ittikafi a cikin Masallaci, kuma ana iya saduwa da ita.
- Fadima ‘yar Abi Hubaish, Allah ya yarda da ita ta ce: “Ya Manzon Allah, ni ina jini ba na tsarkaka, shin zan bar salla ne? Sai Manzon Allah ya ce: “a’a, ... idan hailar ta zo, to ki bar salla,idan kuma ta kau, to ki wanke jinin kiyi salla”.
- Sai dai mai jinin cuta tana yin alwala lokacin shigar kowacesalla.